# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kowa dabam Allah ya yi shi: Mutunta haƙƙin tsirarru

## Kashi na biyar: Sana'ar tuƙi – kallabi tsakanin rawuna a ƙasar Uganda

| | |
|---|---|
| Wadda ta rubuta: | Leylah Ndinda |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |

**'Yan Wasa:**

Mai ba da labari

| | |
|---|---|
| Stella Mary Nampidja: | 'yar shekara 25 |
| Abbey Lulemiro: | ɗan shekara 40 |
| Anthony Wesaka: | ɗan shekara 30 |
| Patience Atuhaire: | 'yar shekara 35 |

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa da ku a kashi na biyar cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" mai bayani a kan mutane marasa rinjaye a cikin al'umma, da batun mutunta haƙƙinsu, da kuma yaƙar nuna musu bambanci a Afirka. Ko da yake mata kwata-kwata ba sa cikin marasa rinjaye a al'umma, sai dai wannan ba ya nufin ana ba su damar yin wasu abubuwa daidai da maza. A sassa da dama na duniya ba wai Afirka kaɗai ba mata dai sai sun tashi sun nemi haƙƙoƙinsu. Yawanci sukan samu kansu a matsayin koma-baya, musamman wajen yin wata sana'a ko samun wani aiki. A yau shirin namu zai kai mu zuwa Kampala ne, babban birnin ƙasar Uganda. Ba baƙon abu ba ne ka ga mata na tuƙa mota a nan, amma baƙon abu ne ka gan su suna tuƙa motar kamfani. Za mu gana da wata matashiya ne wadda ta tari aradu da ka.

**Mai ba da labari:**

Yau rana ce ta Alhamis kimanin ƙarfe ɗaya, ga rana ta take. A irin wannan yanayi ne mutum kan so ya ɗan samu ya sanyaya jikinsa a 'swimming pool' saboda zafin rana. Amma ba kowa ne yake samun irin wannan damar ba saboda aiki ya yi wa kowa yawa, kowa yana bakin aiki.

Ba a yin dai wata cikakkiyar harka a wannan wajen ajiye motoci na kamfanin 'Monitor Publications' da yake Namuwongo wadda wata unguwa ce a wajen garin Kampala. Ga wasu maza guda uku can da mace ɗaya suna zaune a kan benci suna hirar ya da rana. Waɗanann bencina wani agaji ne da 'Monitor Publications' suka yi wa direbobinsu: an sa su ne a wasu rumfunan kwano don direbobin su samu warin fake wa zafin rana yayin da suke jiran aikin da za a sa su.

A kan irin waɗannan bencina ne na haɗu da Stella Mary Nampidja. Stella ita ce ta huɗu a ɗakinsu, fara ce, kuma tsawonta ya kai kimanin ƙafa biyar da ɗigo uku. Shekarunta 25, tana da sassanyar murya, ga kuma kwarjini. Stella ta karanta Fasahar Sadarwa ne a wata kwaleji mai suna 'APTEC' da ke Kampala. To ko me ya sa ta yanke hukuncin yin sana'ar tuƙi?

**Bayanin Stella Mary Nampidja:**

"*Na zaɓi sana'ar tuƙi ne saboda ina sha'awar tuƙin."*

**Mai ba da labari:**

Sai wani murmushi ya bayyana a fuskar Stella yayin da ta fara bayanin dalilin da ya ja hankalinta ta zama direba.

**Bayanin Stella Mary Nampidja:**

*"Abin da ya ja hankalina na shiga tuƙi shi ne: duk lokacin da ba na komai nakan je kallon tseren motoci kamar dai yadda direbobi kan yi. Wannan shi ne ya ja hankalina na fara tuƙi. Sai na fara tunanin: "Anya zan iya irin wannan tuƙin kuwa?" Daga nan sai na ce, to bari na zama direba a wani kamfani. Ba mamaki nan gaba ni ma zan iya shiga tseren motoci."*

**Mai ba da labari:**

Stella ba ta yarda da cewa rashin aikin da da ma maza ne kan yi zai hana wata mace samun aiki ba. Ta yi bayani cewa, bayan da ta kammala karatun babbar diplomarta sai ta ga an sa tallan wani aiki a ɗaya daga cikin jaridun ƙasar, wato 'Nation Courier Uganda'. Wani reshen kamfanin 'Daily Monitor Publications' ne yake neman direbobi. Ita wannan jarida ta 'Nation Courier' wani ɓangare ne na 'Nation Media Group', ɗaya daga cikin kamfanonin da suke buga jaridu na yau da kullum da kuma na sati-sati, yana kuma da tashoshin talabijin da na rediyo a gabashi da tsakiyar Afirka.
Stella dai sai ta miƙa takardarta ta neman aiki, amma ba ta samu amsa daga 'Nation Courier' ba har kusan wata uku. Daga ƙarshe dai sai aka kira ta gwaji wata rana. Abbey Lulemiro shi ne mai kula da ma'aikata na kamfanin, wato 'supervisor', ga kuma abin da ya ce game da irin yadda gwajin nata ya kasance.

**Bayanin Abbey:**

*"Ta ci, har ma ta ɗara mazan da suka nemi aiki tare. Daga nan sai muka gana da ita, nan ma ta zo ta huɗu. Da ma mutum takwas muke nema, sai kawai muka ɗauke ta."*

**Mai ba da labari:**

'Supervisor' Lulemiro ya yi bayanin yadda sauran direbobi da ma'aikatan kamfanin suka yi yayin da suka ji cewa an ɗauki direba mace.

**Bayanin Abbey:**

*"Yawancinsu sai suka yi ta murna suna cewa, "Sun ɗauki mace, sun ɗaki mace!". Kowa ya ƙagara ya ga yadda za ta yi aikin. Anya kuwa za ta iya tuƙin? Dalili kuwa shi ne, mu a nan muna da wani tunani na shakkar ko mace za ta iya tuƙa mota 'manual'. Kowa so yake juyin aiki ya haɗa su da ita don dai ya tabbatar da cewa za ta iya aikin, don kuwa duk sun ɗauka cewa aiki ne mai wahala kuma mace ba za ta iya ba. Sun kuwa taimaka ta wannan hanyar."*

**Mai ba da labari:**

Stella ba ta da wani ƙorafi game da yadda abokan aikinta maza suka karɓe ta.

**Bayanin Stella:**

*"Akwai kyakkyawar dangankata tsakanina da direbobinmu maza saboda ni kaɗai ce mace a wannan ɓangaren. Suna taimaka mini idan wani abu ya fi ƙarfina. Gaskiya suna kula da ni sosai."*

**Mai ba da labari:**

Watan Stella uku ke nan tana wannan aikin. Ita kaɗai ce direba mace da take aiki a kamfanin 'Nation Courier Uganda'. Aikinta ya haɗar da kai masu kawo rahotanni da kuma ɗauko su bayan sun gama aikinsu, da kuma rarraba jaridu da saƙwanni zuwa sassa dabam-dabam na Uganda.

**Bayanin Stella:**

*"Tuƙi ba abu ne mai sauƙi a wurin mace ba. A ɓangaren da nake ba dama mutum ya zauna ya huta. Sai ka ji an ce da kai za ka kai jarida Kasangati, daga nan kuma ka dawo, kafin ka zauna an ce da kai za ka kai mai ɗauko rahoto Mulago, ka kai shi ka dawo. Akwai gajiya, amma duk da haka ina son aikina."*

**Mai ba da labari:**

Stella ta yi bayani cewa, gudunta ba ya wuce kilomita 120 a kowace sa'a. Ba ta gamuwa da matsaloli sosai a kan hanya. Babban ƙalubalenta a wannan harka shi ne: cunkoson motoci, da rashin kyan hanya waɗanda su suke rage mata tafiya. Ta fahimci cewa lokaci abu ne mai muhimmanci a wajen 'yan jarida, don haka tana ɗan ƙagara idan aka samu cunkoson motoci wanda kan sa 'yan jarida su makara a kan irin ayyukan da ake ba su. A lokacin da muka kammala ganawarmu da Stella, da ma ana ta jiranta. 'Supervisor' ɗinta, Abbey Lulemiro, ya ba ta wani aikin.

**Bayanin Abbey:**

*"Stella, ga wannan mutumin. Zai je Bugolobi, KK security ne."*

**Mai ba da labari:**

Tun da yanzu Stella ta tafi, bari mu tattauna da wasu daga masu ɗauko rahoto don mu ji ta bakinsu game da irin tuƙin da Stellar take yi.

**Bayani wani mai ɗauko rahoto – Anthony Wesaka:**

*"Na lura tana kula da danjar ba da hannu, kuma ba ta yin 'overtaking' kamar yadda abokan aikinta maza ke yi. Akwai ababen hawa da yawa a cikin garin, don haka idan mutum ya rufta za a rufta da shi. Irin wannan tuƙin nata yana kawo mana cikas, saboda mu muna gaggawa don mu ɗauko rahoto, ita kuma ba ta gudu don haka mutum na iya rasa wani labarin, sai dai kuma za ka isa lafiya. Ka ga kuwa ina amfanin baɗi ba rai!"*

**Mai ba da labari:**

Idan da za a ce su zaɓa, shin waɗannan 'yan rahoton za su fi so direbobi maza su tuƙa su ko kuwa Stella?

**Bayanin Anthony Wesaka:**

*"Saboda yanayin aikinmu zan fi so namiji ya tuƙa ni, don wani lokacin akwai buƙatar sai ka yi hanzari don kada a yi wani abin ba ka nan ta yadda ba za ka*

*samu cikakken bayani ba. Idan kai mai ɗaukar hoto ne, ba za ka ɗauki wani abin da aka yi idan ba ka nan ba. Don haka zan fi son direbobi maza, amma idan ina ɓangare da ya shafi zama a ofis ne, to zan fi son Stella ta tuƙa ni tun da ba wani sauri nake yi ba, kuma ga shi tana kula da dokokin hanya."*

**Mai ba da labari:**

A ƙasashen Afirka da dama mata na da dalilin yin ƙorafin cewa ana nuna musu bambanci a wajen aiki ko kuma a makaranta. Amma ba haka abin yake ba a Uganda.

Kamar yadda Rahoton Ayyukan Ci-gaba na Majalisar Ɗinkin Duniya Reshen Uganda ya nuna, tun shekarar 1990 ƙasar Uganda ta yi rawar gani wajen ɗaukar mata a jami'o'i da sauran makarantun gaba da sakandare na ƙasar. Ana ɗaga wa matan da suke neman shiga makarantu ƙafa don dai su samu shiga. Wannan tsarin ya ƙara yawan matan da suke samun damar shiga jami'o'i sosai.

Kundin Tsarin Mulkin ƙasar ta Uganda ya ƙunshi sassan da suke kula da ba wa mata dama a kowane mataki, har ma da na shugabanci. Misali, kowace gunduma a Uganda na da wakiliya wadda babban aikinta shi ne, lura da duk wasu matsalolin da suka shafi matan da suke yankin nata.

Saboda yawan matan da ake samu suna kammala karatun jami'a, da sauran manyan makarantu, yana da wuya ka ji ana nuna wa mata wani bambanci a matsayinsu na mata. Wataƙila shi ya sa Stella ba ta da matsalar yin aiki tare da maza. Shugabansu Abbey Lulemiro yana yaba mata a ko da yaushe.

**Bayanin shugaban su Stella – Abbey Lulemiro:**

*"Tana da kazar-kazar wajen aiki, ba ta da kasala, kuma tana jin daɗin aikin tuƙin. Da farko na ɗauka ta zo ne ta fara aikin tuƙin, sannan ta gani ko akwai wani aikin da za ta samu a wani ɓangaren, na ma yi mata wannan tambayar lokacin da muka gana da ita. Sai ta ce, "A'a, ko da ma zan yi wani aikin, na zo na yi aikin tuƙi ne, saboda na fi son tuƙin". Sai na tambaye ta, ko wane irin aiki za ta iya? Sai ta ce, aikin tara bayanai. Wani lokacin nakan sa ta aikin tara bayanai saboda ta iya shi. Takan shigo ofis ta taimaka mini idan ba wani aikin tuƙi da za ta yi."*

**Mai gabatarwa:**

Muna fatan kun ji daɗin sauraron wannan labari na wannan mata direba ta birnin Kampalan ƙasar Uganda. Wadda ta kawo wannan rahoton ita ce Leylah Ndinda. Idan kuna son sake sauraron wannan shiri ko kuma wasu daga cikin shirye-shirye a kan mutane tsirarru da yaƙar nuna musu bambanci da ake yi a Afirka, sai ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Muna kuma marhabin da ra'ayoyinku waɗanda za ku iya aiko mana ta shafinmu na 'Facebook'. Ku kasance lafiya.